

Tabbacin Albarku da La'anoni

An mai da Yesu la'ana domin mu sami albarkar



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

An mai da Kristi la'ana a kan gicciye domin mu sami cancanta da kuma karɓar albarkar. Domin karɓar wannan tanadin da Allah ya yi mana, ya zama dole mu fahimci yanayin na albarkun da la'anonin. Idan ba mu fahimci waɗannan kalmomi guda biyu ba, ba za mu iya ba da kan mu domin amfana daga tanadin Allah ba.

Da albarka da la'ana duka muhimman abubuwa ne a Littafi Mai Tsarki. Kalmar nan "sa albarka" ko "albarka" ta bayyana fiye da sau 410 a cikin Littafi Mai Tsarki; kalmar nan "la'ana" ta bayyana kusan sau 160. Wato, Littafi Mai Tsarki yana da abubuwa da yawa da zai faɗa game da dukan su biyun. Dukan su gaskiya ce - tabbatacce ne tun da aka mai da Yesu la'ana domin a fanshe mu daga la'ana mu kuma sami albarkar.

Waɗansu mutane na iya tunanin cewa albarka gaskiya ce amma la'ana ba gaskiya ba ce, ko kuma zato ne. Wannan ra'ayi ne marar ma'ana. Idan muka yi la'akari da duk wani abu guda biyu mai akasi da juna, za mu iya cewa idan ɗaya gaskiya ne, to, dole ne ɗayan ya zama gaskiya. Misali, ɗauki dare da rana. Idan rana gaskiya ce, to, dare ma gaskiya ne. Zafi da sanyi—idan zafi gaskiya ne, to, sanyi ma gaskiya ne. Nagarta da mugunta—idan nagarta gaskiya ce, to, mugunta ma gaskiya ce. Ba za mu iya yarda da ɗaya mu kuma yi watsi da ɗayan ba. Haka yake da albarku da la'anoni. Albarku gaskiya ne, haka ma la'anoni.

Littafi Mai Tsarki na da abubuwa da yawa da zai koya mana game da yanayin albarku da la'anoni, yadda suke aiki, yadda za ka gane la'ana a rayuwarka, da kuma yadda za a ‘yantar da kai. Idan muka ci gaba da zama da jahilci, wannan zai zama damuwar mu. Za mu rasa yawancin tanadin da Allah ya yi mana ta hanyar mutuwar Yesu ta wurin hadaya a kan gicciye idan muka kasa fahimtar musayarsa ta albarkar da la'ana.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin da ka yi a kan gicciye. Ina furta bangaskiyata cewa albarku gaskiya ne, haka ma la'anoni—tabbatacce ta yadda aka mai da Yesu la'ana domin in sami albarka. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-120-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 09 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.